# RAI NA HAR ABADA



Shirin Allah na asalin ba domin mutum ya mutu ba amma ya rayu har abada. Amma domin zunubi, mutuwa ta shafi dukan yan adam. Bugu da kari, Allah ya aiko da Yesu Kristi Makadaicin Dansa cikin duniya domin ya maidowa mutum da rai. Yanzu kuma mutum zai sake yin rayuwa na har abada (Romans 6:23).

Rai da muke zance, ya fi nufasawa kawai. Yesu yace a cikin Yohanna 10:10 "Barawo bayakan zo ba, amma domin ya sata, da kisa da hallakar; Amma na zo domin su sami rai, su kuma sami shi ayalwa ce." Yesu Kristi yana magana akan wata rayuwa wadda tana canza al'adar mutumtaka daga zunubin zuwa rayuwar adalci. Yesu yana nufi akan rai mai tamani da ta fi rayuwar nama dajini wadda na lokaci kadan da zunubin Adamu ya lalatar. Zunubin Adamu ta shafidukan yan adam ta wurin al'adar.

Zunubin da mutuwa, kowane mutum an haife shi mai zunubi ko da ace yayi laifi ko bai yi laifiba.Shi yasa Kalmar Allah tana nuna mana cewa dukan mutane sun kasa ga darajar Allah ta wurin zunubi wadda hakinta shi ne mutuwa, wannan yana nufi da cewa dukan mu mun dace da mu mutu domin zunubi (Romawa 3:23; 6:23). Amma Allah ya aiko da Yesu Kristi Dansa a cikin duniya ya mutu domin mutum ya sami tsira na har abada. Sabo dahaka duk lokacin da mutum ya tuba zai sami rai na har abada; rai irin ta Allah. Mutum zai zama sabuwar halita idan ma ya mutu zaya dawama da Allah har abada abadin. Mutuwa ta jiki ta zama kamar kauracewa zuwa wata rai.

1 Yohanna 5:9-13 yana da gargadin mai kyau. "Idan mu karba shaidar mutane, shaidar Allah tafi girma: gama wannan shine shaidar Allah da yi akan Dansa. Wanda ya gaskanta da Dan Allah yana da shaidar nan cikin sa: wanda baya gaskanta da Allah ba ya mad da shi makaryaci; domin baya gaskanta da shaidar Allah akan Dansa ba. Wannan shine shaidar, cewa Allah ya ba mu rai na har abada, wannan rai yana cikin Dansa. **Wanda yana da Dan yana da rai wanda ba shi da Dan Allah ba shi da rai.** Wadan nan abubuwa na rubuto maku domin ku bada gaskiya ga sunar Dan Allah; domin ku sani kuna da rai na har abada, domin kugaskanta da sunar Dan Allah". Wannan nassi ta zama shaida ga dukan mutane wadan da sun zabi jaharnama domin sun ki su gaskanta da bishara da suka ji. Wannan afilitana shaida Idan ka ki Yesu Almasihu wannan na nufi ka ki rai na har abada! Yesu yace cikin Yohanna 14:6. "Nine …Rai."

Sa'anda mutum ya karba rai madawami, ya karbi mafificiyar al'ajibi da ta fi saura duka. Madawamin rai shine abu kacal da za shi kawo al'adar uhuhiya (Allah). Akashin gaskiya, kowane mutum zai yi rayuwar na har abada, ko ya zama rayuwa na har abada da Allah, ko kuma har abada da Ibilis da yan koransa a cikin wutar jahar-nama wadda ana kira mutuwa na har abada . Amma Allah yana baka wannan rai madawami yau ta wurin Dansa Isa Almasihu. Abin da zaka yi shine ka karba wannan kyauta.ko za ka karbe shi?.Dukan wanda ya gaskanta da Yesu Kristi yana da rai na har abada, ko da shi tsofo ne ko matashi, babba ko karami, mai arziki ko talaka, ko da menene da yayi a rayuwar ko ya dandana (Yohanna 3:15).

Ba son Allah domin wani ya hallaka ba amma domin dukan mutane su zo su tuba. Aboki, abin da kana bukuta ba shine domin ka canza halinka ba, ko kuma ra'ayin ka ba, ko kuma al'adar ka ba; akashin gaskiya ba sai ka dai-na yi zunubi domin ka cancanta wannan rai ba. A'a! Abin da kana bukuta shi ne maya haifuwa – sabon rai. Ba zaka iya nasara da zunubi ta wuriniyawar mutumtaka ba domin iyawar mutum na da karshe a wannan jiki, amma zunubi abu ne na ruhaniya daya na bukuta a magance ta a ruhaniyance.

Ka zo wurin Allah a yadda kake, yana son ka a yadda ka ke, yana jiranka ayau domin kayi zabi wada zata canza rayuwarka ayau. Yana so ya canza halaya na zunubi acikin ka da zaya kawo mutuwa ya baka rayuwa tasa ta adalci wadda ke haifar da rai madawami (Romawa 6:23, 2 Kor 5:21) zaka soma yin rayuwa irin rayuwar Allah daga yanzu zuwa rana daza ka gan shi ido da ido. Sa'anda an maya haifuwar ka, sharian rai zai fara yin aiki acikin ka, zai yantar da kai daga zunubi da mutuwar ruhaniya (Rom. 8:1,2).

Yesu yace, Hakikka hakika, ina gaya maku, duk wanda ya ji maganar ta ya kuma gaskanta da ni, yana da rai na har abada, ba kuwa za yi masa sharia ba, amma ya ketare mutuwa zuwa rai Yahaya 5:24. Saboda haka, idan ba rigaya ka karbi wannan rai na har abada ba, zai iya zama naka kai tsaye yanzu! Ka dai yi wannan addu'a mai sauki amma mafi muhimmanci kwarai yayin da ka yi shi da gaskiya a cikin zuciyarka:

*"Ya Allah, na gode maka domin ka badda Danka Yesu Kristi ya mutu domin zunubai na, wadda yasa na zama magadan rai na har abada maimakon mutuwar madawami. Na furta Yesu Kristi ya zama ubangiji da mai ceto na, na kuma badda gaskiya a cikin zuciyata ka tashe shi daga mattatu domin in kubuta. Bisa ga maganarka, na furta na sami ceto, an maya haifuwa ta, yanzu ina da rai na har abada. Ina rokon ka ka cika ni da Ruhu mai Tsarki domin ya taimake ni in sadu da shirin ka na rai na abada. Na gode maka uba, acikin sunar Yesu Amin!"*

Na tayi ka farin ciki! Maraba da zuwa cikin iyalin Allah. Yana da muhimmanci ka sami Littafi mai Tsarki, kana karantawa da yin addu'a kullayomi ga uban ka na sama. Ka rika sujada Ikklisiya da ke koyas da Littafi mai Tsarki. Zaka iya sadu da mu domin mu taimake da takardu da zasu karfafa bangaskiyar ka cikin Almasihu.

---

Domin ka sami irin wadan nan yan takardu da zasu taimake ka yin bishara ga wadansu da kuma bukatar bayani, sai ka tuntube adireshi:


LCM

**LIFE COMMISSION MINISTRY**

+23470-32138935, +23480-59153304

P. O. Box 8272, Anglo-Jos, Plateau State, Nigeria

www.lifecommission.org / lifecommission@yahoo.com